# Surah 001: The Key (AlFatehah) - سورة الفاتحة

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ١

[1:1]  Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.

ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ٢

[1:2]  Godiya ta tabbata ga ***ALLAH,*** Ubangijin talikai.

ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ٣

[1:3]  Mafi rahamah, Mafi jinqai.

مَٰلِكِ يَوْمِ ٱلدِّينِ ٤

[1:4]  Mamallakin ranar Sakamako.

إِيَّاكَ نَعْبُدُ وَإِيَّاكَ نَسْتَعِينُ ٥

[1:5]  Kai kadai muke bautawa, kuma Kai kadai muke neman taimako.

ٱهْدِنَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلْمُسْتَقِيمَ ٦

[1:6]  Ka shiriyad da mu ga hanya madaidaiciya.

صِرَٰطَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمْتَ عَلَيْهِمْ غَيْرِ ٱلْمَغْضُوبِ عَلَيْهِمْ وَلَا
ٱلضَّآلِّينَ ٧

[1:7]  Hanyar wadanda Kayi wa ni'ima, ba wadanda aka yi wa fushi ba, kuma ba batattu ba.

.

**1:1 Ayah ta farko a cikin Alqur'ani, watau 'basmalah', ita ce tushen da aka gina mu'ujizan asirin lissafin Alqur'ani mafi a'ala, watau lamba 19. Wannan ayah wanda yake da muhimmancin gaske ta qumshi haraffan larabci 19; kuma an maimaita ko wacce kalma a cikinta a cikin Alqur'ani gaba daya, sau 19 ne (dubi shafuka 1 da 9 domin qarin bayani).*

**1:1-7 Suran farko, watau Al-fatehah, baiwa ce daga wurin Allah da ya baiwa bi'Adama domin ya tabbatar da mun sami ganawa da Shi wurin yin Sallah. An qarfafa wannan tabbacin da abin al-ajabi, mai farfashe duniya da sauqin fahimta-amma da gagarin kwaikwayo ta hanyan ilmin lissafin talifi, wanda ya qalubalanci manyan shehunan ilmin lissafin duniya, ya rikitad da su suka rasa kan ta; ke nan, asirin riyadiyan Alqur'ani watau shifran Alqur'ani ta wuci abin iyawan mutum da nesa ba kusa ba.*

*(1) Lambar suran Al-fatehah 1, aka jera ta da lambobin ayoyin ta 7, jere da juna zai bada: 1 1 2 3 4 5 6 7. Wannan jerin lambobin ninkin 19 ne (19 x 591293).*

*(2) In kuma muka sauya da jerin lambobin harafi ga ko wacce ayah maimakon labobin ayah, za mu samu: 1 19 17 12 11 19 18 43. Wannan jerin lambobin ninkin 19 ne shima.*

*(3) Idan muka gwaba jimlan 'Abjad', watau nauyin ko wacce harafi na kowace ayah ta Al-fatehah, za mu samu:1 19 786 17 581 12 618 11 241 19 836 18 1072 43 6009. Shima wannan lambar ninkawan 19 ne.*

| *Lamban Ayoyi.* | *Lamban Harafi* | *Nauyin Harafi* |
|---|---|---|
| *1* | *19* | *786* |
| *2* | *17* | *581* |
| *3* | *12* | *618* |
| *4* | *11* | *241* |
| *5* | *19* | *836* |
| *6* | *18* | *1072* |
| *7* | *43* | *6009* |
| *Jimla* | *139* | *10143* |

*(4) Lambar da yake nuna wata qumshi dukkan iyakan Surah ta 1, watau Al-fateha, kuma tana da digo 38 (19x2).*

*(5) In muka lura kuma, wannan adadin sifiri 38-jadawali ne na 19 har wa yau. In kuma muka rubuta su kashi-kashi da baya, daga dama zuwa hagu,irin ta rubutun Arabiya, kamar: 6009 43 1072 18 836 19 241 11 618 12 581 17 786 19 1 shima wannan ribawan 19 ce.*

*(6) Kamar yadda muka ambata daga baya, misalin asirin lissafin Alqur'an mai ban mamaki sun taimaka wurare masu yawa da lissafi masu ban mamakin ikon Allah don su tabbatar mana da dukkan daki-daki Sallolin mu (shafi 15).*

*(7) Akwai kuma sauran lissafi na ban mamaki cikin shafi ta daya. Ta haka ne mai karatu, tun daga farko, zai san yana riqe ne da haqikanin littafin shaida cewa wannan saqo ne daga wurin Allah zuwa ga dukkan talikai.*